**JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA** **١٥ Sha'aban, 1443**

**MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI** **1٨ Maris. 2022**

## HAƊIN KAN 'YAN ƘASA WAJEN TUNKARAR MATSALOLI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa :**(Ku yi taimakekeniya akan yi wa Allah biyayya da tsoron Allah)** [al- Ma'ida: 2], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai wayayyiyar al'umma, mai kuma daraja, al'umma ce da mutanen cikin suke a matsayin tsintsiya maɗaurinki ɗaya, suna taimakekeniya a tsakaninsu, suna tallafa wa marasa shi, musamman a lokutan da aka shiga cikin tsanani da rashi, lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya sifanta irin wannan al'umma mai daraja da falala da cewa: **(Misalin muminai wajen soyayya, da tausayi da jinƙan junansu tamkar jiki ne guda ɗaya, wanda idan wata gaɓa ta sami tangarɗa dukan jikin yakan kamu da rashin samun barci da zazzaɓi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Shi dangantakar mumini da mumini tamkar gini ne da kowane sashe yake ƙarfafar ɗan uwansa, sai ya shigar da yatsunsa cikin juna).**

Lallai fahimtar matsaloli da kyautata yin ta'amuli da su abu ne da yake buƙatar haɗin kai tsakanin 'yan ƙasa, da nemo

hanyoyi masu dama, irin su: Ƙaurace wa dukan nau'o'in algushi, da ɓoye kayan buƙatar mutane saboda su yi tsada, da yin amfani da buƙatun mutane wajen azurta kai, lallai addinin mu mai girma ya yi kakkausar hani akan waɗannan munanan cututtuka, Allah ya hana dukan nau'o'in algushi, hasali ma farkon ayoyin da suka sauka a Madina su ne: **(Halaka ta tabbata ga masu tauye mudu. Su ne waɗanda idan za su auni kaya daga mutane suke cika mudu har ya yi tsororiya. Idan kuma su za su aunar wa mutane sai su cuce su ta hanyar tauye masu haƙƙoƙinsu. Shin waɗannan masu tauye mudu ba su tunanin cewa lallai za a tashe su bayan mutuwa ne. A wata rana mai tsananin ban tsoro. Ranar da mutane za su tashi zuwa ga Ubangijin talikai domin fuskantar hukuncinsa)** [al- Muɗaffifina: 1 -6], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗi ta bakin Sayyiduna Shu'aib (AlaiHis Salam) cewa: **(Ya ku mutane na, ku cika mudu da sikilan abubuwan da kuke sayarwa cikin adalci da daidaito, kada ku tauye haƙƙoƙin mutane cikin abubuwansu da suka saya, kada ku yi zalunci da ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar satar dukiyoyin mutane, ko kai masu hari, ko tare hanya da fashi da makami, inda zai zama kun ɗauki sata ta zama hanyar neman abinci da shari'a ba ta amince ba)** [Hudu: 85], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya yi mana algushi ba ya cikinmu).**

Haka ma shari'ar Musulunci mai daraja ta hana dukan nau'o'in ihtikari (ɓoye kayan buƙatar saboda ya yi tsada), da yin amfani da buƙatun mutane; saboda yin hakan wasa ne da abincin mutane, da kuma ginshiƙin rayuwarsu, da kuma yin masu baba-kere; kawai saboda tara haramtacciyar riba, wadda ake samun bayan an gallaza wa mutane, Allah mai girma da ɗaukaka yana

cewa: **(Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, kada wani sashe naku ya ci dukiyar wani sashe ba tare da haƙƙi ba, sai dai ya halatta ku yi kasuwanci a tsakanin ku, ta hanyar yarda, kada ku yarda ku halakar da kawunanku ta hanyar saɓa wa umurnin Ubangijnku, kada wani ya yarda ya kashe ɗan uwansa, babu wani rai da yafi wani, lallai Allah mai yawan tausayinku ne a koda yaushe)** [an- Nisa'i: 29], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Sam bai halatta Musulmi ya zubar da jinin Musulmi, ko ya ci dukiyarsa, ko ya ci mutuncinsa ba),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Babu mai ɓoye kayan amfanin mutane saboda su yi tsada sai mai kuskure)**, shi mai ɓoye kayan amfani da buƙatar mutane mutum ne da ba shi da dattako, balle kishin ƙasa; saboda ya fifita son kansa akan addini, da ƙasa, da mutuntaka; a dalilin haka ne ya cancanci Allah mabuwayin sarki ya yi fushi da, haka ma sauran mutane su ƙi shi.

Lallai da mai ɓoye kayan amfani da buƙatun mutane saboda su yi tsada, da mai yin amfani da buƙatarsu wajen biya wa kansa buƙatunsa na son zuciya za su san azabar da aka tanadar masu a ranar alƙiyama da su da kansu sun nesanci wannan zalunci da suke yi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Duk wanda ya yi ha'inci, zai zo da zunubin abin da ya yi ha'incin a ranar alƙiyama..)** [Ali Imran: 161], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Allah yana azurta mutumin da yake sayo kaya daga nesa ya kawo kasuwa, yana kuma tsine wa wanda yake ɓoye kayan buƙatun mutane saboda ya yi tsada)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Bawan dinare da dirhami ya taɓe).**

Shi kuwa ɗan kasuwa mai kishin ƙasa, kuma mai gaskiya, shi ne wanda ba ya yaudara, ba kuma ya algushi, ba kuma ya ha'inci; hasali ma kishin ƙasarsa ne yake ɗaukansa zuwa ga rage yawan ribar da yake samu saboda ya sauƙaƙa wa mutane, musamman a lokacin da matsaloli suke faruwa, kuma babu shakka hakan yana cikin tausayi da jinƙan da ake samun lada saboda su, lallai Allah mai girma da buwaya ya yi wa ɗan kasuwa mai gaskiya alƙawarin babban lada ta bakin Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), inda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yake cewa: **(Lallai ɗan kasuwa mai gaskiya kuma amintacce yana tare da Annabawa, da siddiƙai, da shahidai),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Allah ya yi rahama ga mutumin da yake rangwame idan zai sayar, da idan zai saya, da idan zai biya bashi).**

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai akwai buƙatar bayyanar ɗabi'ar fifita wani akan kai a lokacin faruwar matsaloli, ba amfani da buƙatun mutane wajen azurta kai ba, haka ma ana buƙatar ɗabi'ar tausayi ne ba ƙeƙashewar zuciya da son kai ba, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk mutumin da ya kwana a ƙoshe, makwabcinsa kuma ya kwana da yunwa alhalin yana sane da haka, to bai yi imani da ni ba)**, lokaci ne da ake buƙatar bayyanar jinƙai da bayar da kyauta da baiwa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Suna kuma gabatar da buƙatun waɗanda suka yi hijira akan buƙatun kawunansu, koda kuwa suna tsananin**

**buƙata. Duk wanda aka kiyaye shi –da kiyayewar Allah- daga barin tsananin ƙwauron zuciyarsa, to, lallai su ne suke da babban rabo cikin duk abin da suka so)** [al- Hashri: 9], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai idan abincin ƙabilar Ash'arawa ya tashi ƙarewa a lokaci yaƙi, ko abincin iyalansu ya yi ƙaranci a garin Madina; sai su tattara dukan abin da suke da shi a tufafi ɗaya, sannan sai su raba mudu mudu daidai wa daida a tsakaninsu, su nawa ne, ni ka nasu ne).**

Babu shakka haɗin kai da taimakon juna abubuwa ne da suke taka babban rawa wajen ƙarfafa rayuwar zamantakewa da ta mutuntaka, suna haɓaka soyayya da ƙauna tsakanin al'umma, saboda haka ne Shari'ar Musulunci mai daraja ta kwaɗaitar da yinsu, Allah mai girma yana cewa: **(Ku yi taimakekeniya akan yi wa Allah biyayya da tsoron Allah, kada ku kuskura ku yi taimakekeniya wajen saɓon Allah da zalunci..)** [al- Ma'ida: 2], lallai wannan haɗin kai da taimakon juna suna bayyana ne ta hanyar ciyar da dukiya a hanyoyin alhairi, musamman ciyarwa wajen samar da abinci da toshe yunwar mabuƙata talakawa, lallai Allah mai girma da ɗaukaka ya sifanta bayinsa masu tsoron Allah da cewa: **(Suna kuma ciyar da abinci -duk da suna so suna kuma matuƙar buƙatarsa- ga matalaucin da ya gajiya wajen nema, da ƙaramin yaron da ya rasa mahaifansa, da fursinan yaƙin da ba ya mallakar komai. Suna kuma faɗi a cikin zuciyarsu cewa: muna ciyar da ku ne kawai saboda biɗar yardan Allah, ba ma son ku ba mu wani abu a maimakonsa, ko ku yi mana kyauta, haka ma ba ma son yabo daga gareku. Mu muna tsoron Ubangiji ne game da wata rana da fuskoki a cikinta za su yi matsanancin murtukewa. Sai kuwa Allah ya katange su ga**

**barin tsanance-tsanancen wannan rana, a sa'ilin da fuskokin kãfirai suke murtukewa, sai Allah ya haskaka fuskokinsu, ya kuma sanya farin-ciki da annashuwa a cikin zukatansu. Saboda haƙurin da suka yi ne Allah ya saka masu da aljanna da mulkin da yake da daɗi, ya kuma ba su tufafi na alhariri mai taushin taɓawa )** [al- Insan: 8 -12], haka ma Maɗaukakin Sarki ya sifanta mutane na gari da cewa: **(Ko ciyarwa a lokutan da ake fama da yunwa. Marayan da ake da kusanci da shi a taimaka masa; saboda zumunta da kuma rashi da yake fama da shi. Ko miskini da yake halin buƙata da rashi)** [al- Balad: 14- 16], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa**: (Ku ciyar da abinci, ku kuma sadar da zumunci, ku kuma yi sallah da daddare lokacin da mutane suke barci, sai ku shiga aljanna cikin aminci)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Zaɓaɓɓe a cikinku shi ne wanda ya ciyar da abinci).**

**Ya Allah Ubangiji ka kare mana ƙasarmu da sauran ƙasashe baki ɗaya.**